# MAULIDI; TARIHIN SA DA HUKUNCIN SA

NA

ABU ABDILLAH
ALIYU IBRAHIM MUHAMMAD
(ALMAJIRI ALKAFAWEE)

BITA:
DR. IDRIS ZUBAYR ATTUNGAWEE

# MAULIDI;
# TARIHIN SA DA HUKUNCIN SA

NA

ABU ABDILLAH
ALIYU IBRAHIM MUHAMMAD
(ALMAJIRI ALKAFAWEE)

BITA:
DR. IDRIS ZUBAYR ATTUNGAWEE

**BIKIN MAULUDI; TARIHIN SA DA HUKUNCIN SA**

**GABATARWA:-**

Da sunan Allah Mai yawan Rahama Mai ikon isar da RahamarSa zuwa ga bayinSa.

Godiya su ƙara tabbata ga Allah Mahaliccin talikai.

Salati da sallamawa ga fiyayyen halittar Allah da iyalan sa da sahabban sa da waɗanda su ka bi hanyar sa har zuwa ranar alkiyamah.

Wannan ƴar ƙaramar takarda ce da ta tattara wasu daga cikin maganganun malamai a kan tarihi da hukuncin bikin Maulidi a Shari'ar da Manzon Allah ﷺ ya zo da shi.

Abun da ya jawo hankali na zuwa ga wannan shi ne ganin yadda a ka mayar da harkar bikin maulidi kamar wani asali cikin asalan Shari'ah har ta kai ga wasu suna auna soyayyar mutum musulmi ga fiyayyen halitta da yin bikin Maulidi. In ka na yi to, ka na son sa in kuma ba ka yi to, ba ka son sa ﷺ

Na yi ƙoƙari don ganin cewa ban rubuta wani abu na fahimta ta ba ta ƙashin kai na saboda maganganun da Malamai su ka yi a kai sun wadatar.

Da akwai wani rubutu mai kama da wannan da harshen hausa da na sani ya yaɗu a cikin al'ummar mu na wani malami da ban yi wannan rubutun ba.

Ƙofa a buɗe take don karfan gyara ko ƙari daga duk wani Ahlus-Sunnah.

Allah na ke roƙo da ya amfanar da al'umma da wannan rubutu kuma ya sanya ikhlasi cikin aikin.

**Aliyu Ibrahim Muhammad**

***(Abu-Abdillah Al-kafawee)***

**1445/02/05**

**<u>GIRMAMA ANNABI ﷺ</u>**

((Lallai girmama Annabi ﷺ yana daga cikin ayyukan Muminai da a ka umurce su da shi kuma abu ne da Allah ya ke so, kuma yana daga alamar Imani da sababin samun tsira, kamar yadda Allah ya faɗa cikin Al-ƙur'ani **(Suratul A'araf: 157) da kuma Suratul Fathi: 8-9).**

Nau'ukan abun da ake girmama Annabi ﷺ suna da yawa, kamar son sa, da Imani da shi, da bin sa, da yi masa biyayya, dayi masa Salati a lokacin da a ka ambace shi.

Kuma hanyar sanin yadda a ke girmama shi ﷺ shi ne Nassi tabbatacce daga maganar Allah ko na ManzonSa ﷺ; saboda girmama shi ibada ce, kuma dukkan ibada a na tsayuwa ne a kan dalili.

Idan mutum yayi nufin girmama Annabi ﷺ da wani abu, to ya wajaba ya zama abun da zai girmama shi da shi ya tabbata a Shari'ah, in ba haka ba, abun da zai aikata abun zargi ne.

In ka karanta Hadisin Ibn Abbas wanda Imam An-Nasa'i ya riwaito a Hadisi mai lamba 51, da Hadisin Abu-Huraira wanda Imam Abu-Dawud ya riwaito a Hadisi mai lamba 2042, da Hadisin Umar Ɗan Khattab wanda Imamul-Bukhari ya riwaito a Hadisi mai lamba 3445, da bayanan da malamai su ka yi za ka fahimci abun da ya gabata)). **[Duba: (قلم في تعظيم النبي ﷺ بعمل المولد) na Ash-Shaykh Salih Al-Usaimiy]**

## SHIN MAULIDI NE MA'UNIN AUNA SON ANNABI ﷺ?

Masu bikin ranar Maulidi suna riya cewa yin bikin shine cikar soyayya da girmamawa ga Manzon Allah ﷺ? da cewa ranar haihuwarsa rana ce mai albarka, a wannan ranar ce hasken shiriya ta haska, kuma hasken ta game duniya, kuma Manzon Allah ﷺ ya kasance yana azumtar duk ranar litinin, da a ka tambaye shi sai yace: **(Wannan itace ranar da a ka haife ni kuma a na ɗaukaka ayyukan bayi zuwa sama, sai nake so a ɗaga aiki na ina azumi)**, kuma idan manyan mutane a na yi musu bikin zagayowar ranar haihuwa to, ai Manzon Allah ﷺ shi yafi cancanta da a girmama kuma shi ne mafi girman abun koyi.

Masu kira zuwa ga bikin Maulidi suna riya cewa, wannan tattaunawa ce tsakanin masoya Manzon Allah ﷺ da makiyansa ﷺ, ko saɓani ne tsakanin masu girmama shi ﷺ masu masu ƙasƙanta shi ﷺ.

Babu shakka cewa gabatar da wannan matsalar a wannan yanayin ya na daga cikin mafi girman cakuɗa al'amura da kuma rashin adalci ga mafi yawan al'ummar Musulmi, kwata-kwata matsalar ba haka take ba, waɗanda basa ganin halascin yin bikin maulidi saboda tsoron aikata bid'ah a cikin addini sune mafiya kyawun masu rabo cikin son Manzon Allah ﷺ da yi masa biyayya, su suka fi kowa riƙo da Sunnar sa da tsayuwa a kan abun da ya tabbata daga Hadisan sa, masu bibiyar sa da koyi da shi a kowani hali ﷺ, kuma suka fi kowa sanin Sunnar sa da shiriyar sa da addinin da ya zo da shi.

Ƙin su ga aikata bikin Maulidi da mayar da ranar idi, sun ƙi yarda da hakan ne saboda soyayyar su gare shi da biyayyar su gare shi ﷺ, saboda su din basa so su saɓa ma umurnin shi ﷺ.

Amma Azumin da yake ki ﷺ a kowace ranar Litinin, ai Masoyan sa a gaskiya suna Azumtar wannan rana a kowani sati.

Amma su masu biki suna bikin a duk ranar da ta faɗo kuma sau ɗaya a shekara. **[Duba Littafin: (حقيقة الاحتفال بالمولد النبوي) na Ash-Shaykh Abdurrahman Abdul-khaliƙ].**

**TARIHIN FARA MAULIDI**

((Shi fa maulidi ba a san shi ba a zamunan farko na Sahabbai, basu san shi ba kwata-kwata, basu taɓa tunanin yin shi ba tun asali, haka ma waɗanda suka biyo bayan su (Tabi'ai) da waɗanda suka biyo bayan Tabi'ai da jagororin magabata gabaɗaya, daga cikin su Malaman Mazhabobi guda huɗu shahararru.

Haka ma Malaman Hadisi gabaɗaya sai ƴan kaɗan waɗanda suka rayu bayan ƙarnoni ukun farko, ƙarnoni mafiya alheri, haka ma duk waɗanda suka rayu a irin tafarkin su har zuwa yau.)) **[Duba Littafin: (حقيقة الاحتفال بالمولد النبوي) na Ash-Shaykh Abdurrahman Abdul-khaliƙ]**

Abun tambaya shi ne: Yaushe aka fara, kuma su wa suka fara, kuma menene dalilin su na farawa?

((**Amsa**: Farkon waɗanda suka fara ƙirƙirar wannan aiki (Maulidi) su ne surakunan Daular Fatimiyyah (الفاطمية) a ƙarni na huɗu bayan Hijira, da wanda a ke kira da (المعز لدين الله) amma abun sani shine, shi da mutanin sa gabaɗaya Isma'ilawa ne Zindiƙai, ƴan falsafa, masu tutiyar dangantaka zuwa ga Annabi ﷺ, amma su a haƙikanin zuri'ar Abdullahi Bn Maimun ne bayahude)).

An Tambayi Imam Ash-Shaukāniy a kan Maulidi sai yace: ((Har yanzu ban samu a kan tabbatuwan shi cikin Ƙur'ani da Sunnah, ko ijma'i ko ƙiyasi ko dalili, sai dai ma Musulmai gabaɗaya sun yi ijma'I a kan babu wannan al'amarin a zamanin mafiya alherin mutane, haka waɗanda suka biyo bayan su)) **[Duba Littafin: (رسالة في حكم المولد) na Ash-Shaukāniy].**

((Malamai sun yi saɓani a kan wane ne ya ƙirƙiro bikin Maulidi a maganganu guda biyu; amma wanda yafi inganci shine; wanda suka ƙirƙira sune Ubaidiyyūn waɗanda su ka yi mulki a misra da a ke kuskuren kiran su da (الفاطميون))). **[Duba Littafin: (تظريز رسالة في حكم المولد) na Ash-Salih Al-Usaimiy]**

((Lalle shi (bikin maulidi) bid'ah ne. Saboda bashi da asali a Ƙur'ani ko Sunnah ko ayyukan magabata na ƙwarai waɗanda suka rayu a ƙarnoni mafiya falala, abun sani dai an ƙirƙiro shi ne daga baya bayan ƙarni na huɗu Hijiriyya. Yan Shi'a Fatimiyya suka ƙirƙiro shi)). **[Duba Littafin: (Kitabut-Tauhid) na Ash-Shaykh Salih Al-Fauzan].**

((Lallai tambaya ya yawaita a kan taron da wasu mutane su ke yi a watan Rabi'ul-Awwal da su ke kira Maulidi, Shin ya na da asali a addini? Sai nace: Ban san wani asali ba na wannan aiki na Maulidi, ko a Ƙur'ani ko a Sunnah, kuma babu a al'ummah, wadanda sune abun koyi a addini...)) [**Duba (رسالة المورد في حكم المولد) na Shaykh Tajuddeen Al-Fakahaaniy].**

((Idan hakan ya tabbata (rashin asalin sa daga Ƙur'ani da Sunnah) zai bayyana ga mai nazari cewa lallai duk wanda ya halatta shi (bikin maulidi) bayan ya sallama cewa lallai bid'a ce, kuma (lallai ko wace bidi'a ɓata ce)) da Nassi tabbatacce daga fiyayyen halitta ﷺ to, bai fadi komai ba sai abun da ya saɓa ma Shari'ah tsarkakakke)). **[Duba Littafin: (رسالة في حكم المولد) na Ash-Shaukāniy].**

**HUKUNCIN BIKIN MAULIDI DA BAYANIN ƁARNAR DA KE CIKIN HALATTA SHI.**

((Lallai duk wanda ya ƙirƙiri wani abu ya danganta shi ga addini kuma wannan abun ya zama bashi da asali a addini, to lallai wannan ɓata ne, kuma addini ya barranta daga gareshi)). [Ibnu Rajab Al-Hanbaliy a Littafinsa (جامع العلوم والحكم)].

((Lallai aikin Maulidin Annabi ﷺ ƙirƙirarren al'amari ne, ba zaka samu ambaton shi a Ƙur'ani ko Sunnah ba, kuma babu wani Sahabi da ya aikata shi a garin Madina ko wani garin da ba wannan ba, duk da tsananin soyayyar da su ke ma fiyayyen halitta ﷺ da cikan ilimi da suke da shi a hakkin sa, da tsayuwar da suke wajan kāre haƙƙin nasa, kuma babu wani daga cikin Taba'ai da ya aikata ko waɗanda suka biyo bayan Tabi'ai! Malamai da yawa sun ambaci hakan, daga cikin su akwai Ibnu Taimiyyah da Ibn Hajar da As-Sakhawiy)) **[Duba Littafin: (تظريز رسالة في حكم المولد) na Ash-Salih Al-Usaimiy].**

((Imam Malik (RahimahuLLāh) yace: Duk wanda ya (ƙirƙiri wata bid'ah a Musulunci kuma yake ganin ta mai kyau, to lallai ya riya cewa lallai Annabi ﷺ ya ɓoye wani abu na saƙon da Allah ya aiko shi da shi; duk abun da bai zama addini ba a wancan zamanin ba zai taɓa zama addini ba a yau)) **[Duba Littafin (الاعتصام) na Abu-Ishaƙ Ash-Shaɗibiy].**

Zai bayyana maka ɓarnar mai halatta bikin Maulidi da mayar da shi Shari'ah ta waɗannan fuskokin:

**<u>Fuska ta Farko</u>:** Wannan aikin Annabi ﷺ bai aikata shi ba, kuma bai yi umarni da aikata shi ba, kuma Sahabban sa ba su aikata shi ba, kuma babu wani daga cikin ƙarnoni mafi falala (Ukun Farko) da su ka aikata, idan an tabbatar da hakan, to mai aikata hakan ya shiga ƙarƙashin narkon azabar da Allah ya yi alƙawari ma masu sabawa ManzonSa ﷺ a cikin (Suratun Nisa'I, Aya ta 115).

**<u>Fuska ta Biyu</u>:** Lallai mai kutsawa cikin wannan aiki da ƙoƙarin halatta shi ya na shiga cikin jan kunne da Annabi ﷺ ya yi da ya ce "**kowace bid'ah ɓata ce kuma makomar ɓata ita ce wuta**" [Sunan Abi–Dawud].

**<u>Fuska ta Uku</u>:** Lallai mai aikata wannan aiki babu ladan ko sisi da zai samu, hasali ma aikin abun mayarwa ce a kan sa saboda faɗin Manzon Allah ﷺ "**Duk wanda ya aikata wani aiki wanda babu umurnin mu a ciki to an mayar mas**a" [Bukhari ya riwaito]

**<u>Fuska ta Hudu</u>:** Allah ya faɗa a inda yake cewa "**Lallai a yau na cika muku adinin ku...**" [Suratul Ma'idah]. Wanda ya ke cewa bikin maulidi ibada ce kuma za'a iya bautar Allah da shi, to lallai ya na ƙaryata wannan aya ne, kuma hakan zai iya kai shi ga kafirci.

**<u>Fuska ta Biyar:</u>** Lallai wanda ya ke ƙoƙarin halatta wannan aiki na Maulidi kamar ya na tuhumar Annabi ne ﷺ a kan cewa akwai wani abun kirki da ya ɓoye bai bayyana ba. [Duba maganar Imam Malik da ta gabata].

**<u>Fuska ta Shida</u>:** Lallai cikin aikata wannan bid'a akwai canza asali daga cikin asalai na Shari'ah wacce ita ce son Annabi ﷺ da biyayya zuwa gare shi a fili da ɓoye, saboda waɗanda su ke yin wannan bid'ar suna cewa wannan ya na daga dalilai na fili da suke nuna son sa ﷺ duk wanda baya yi to maƙiyin Manzon Allah ﷺ ne.

**<u>Fuska ta Bakwai:</u>** Lallai a bikin maulidi akwai kamanceceniya da addinin Nasara, waɗanda su ke bikin ranar Haihuwar Annabi Isa (Aminci ya tabbata a gareshi) kuma an hana mu koyi da kamanceceniya da su.

**<u>Fuska ta Takwas:</u>** Lallai cikin aikata maulidi akwai zargi ga waɗanda su ka gabace mu daga Sahabbai da waɗanda su ka zo bayan su wajan nuna cewa mun fi su son Manzon Allah ﷺ da kuma nuna cewa su ba su cika masa hakkin sa da ke kan su ba na soyayya da girmamawa, saboda masu yin bid'ah suna cewa ga waɗanda basa yin tarayya da su ba sa son Annabi ﷺ.

**<u>Fuska ta Tara:</u>** Cakuɗuwan wannan biki da nau'uka kala-kala na manyan zunubbai kamar kade-kade, da raye-raye, da shaye-shayen kayan maye da bayyana wasu nau'uka da sihiri da tsubbace-tsubbace, ya isa ya nuna maka kuskuren wannan aikin.

**<u>Fuska ta Goma</u>:** Cakuɗuwan wannan biki da wasu nau'uka na albazaranci da dukiya da bayar da dukiya a inda bai cancanta ba. **[Duba Littafin: (مولد النبي، تاريخه، حكمه، آثاره ) na Nasir Bin Yahya Al-Hunainiy]**

**RUFEWA:**

((A takaice: Lallai ya wajaba mu fahimci cewa, wannan al’amarin da ya ke bayyana ƙarami a farko amma babba ne sosai a ƙarshe, kafirci ne da zindiƙanci)). **[Duba Littafin: (حقيقة الاحتفال بالمولد النبوي) na Ash-Shaykh Abdurrahman Abdul-khaliƙ]**

((Allah ka sani cewa, lallai ikon mu gajere ne sosai wajen tsayuwa a kan hana wannan ɓarnar, da rushe wannan aiki abin ƙi, babu komai da za mu iya yi sai dai ankararwa da jan hankali da kuma isar da sako, kuma mun yi.

Ya Allah ka kare addini ka, ka tsarkake shi daga dattin waɗannan sheɗanun masu bautar kaburbura, kuma ka kare mu daga wannan dattin) **[Duba Littafin: (رسالة في حكم المولد) na Ash-Shaukāniy].**

((... Kuma bana nufin in saɓa muku zuwa ga abin da nake hana ku daga gare shi. Ba ni nufin komai face gyara, gwargadon da na sami dama. Kuma dacewa ta ba ta zama face daga Allah. A gareshi na dogara, kuma zuwa gare shi na wakkala) **[Suratu Hud: 88].**

Ranar Talata (5-02-1445 A.H/22-08-2023).

***Abu Abdillahi Aliyu Ibrahim Muhammad***

Keffi, Jihar Nasarawa.

# MAULIDI

## TARIHIN SA DA HUKUNCIN SA